Jerin Littafan Shi’a Na 6

# Ahalul Baiti

a mahangar

# ‘Yan Shi’a

da

# Ahalus Sunna

Umar Labɗo

# بسم الله الرحمن الرحيم

## Gabatarwa

'Yan Shi'a suna da'awar son Ahalul Baiti, da ƙaunar su, da jiɓintar su, da yin biyayya a gare su, da koyi da su. Suna iƙirarin cewa wai suna karɓo addininsu daga shugabannin Ahalul Baiti, musamman Sayyidina Ali da Hassan da Hussaini, Allah ya ƙara musu yarda, da kuma jikokinsu waɗanda suke kira Imamai.

A lokaci guda kuma, 'yan Shi'a suna dangana wa Ahalus Sunna ƙin Ahalul Baiti da gaba da su da rashin girmama su. Suna ɗauko abin tun daga tushe, inda suke cewa wai Sahabban Annabi(SAW), Allah ya ƙara musu yarda, sun nuna matuƙar gaba da ƙiyayya ga Ahalul Baiti, sun zalunce su, kuma sun hana musu haƙƙoƙinsu, ciki har da haƙƙinsu na shugabantar al'umma bayan rasuwar Annabi(SAW). Kuma suna ganin daga nan ne Ahalus Sunna, a matsayin su na mabiyan Sahabbai, masu koyi da su, suka gado wannan ƙiyayya da gaba ga Ahalul Baiti.

Manufar wannan littafi, in Allah ya yarda, ita ce warware wannan mas'ala a ilmance, kuma a bisa doron adalci.

Littafin zai yi bayanin ma'anar Ahalul Baiti a mahangar 'yan Shi'a, da yadda suka ɗauke su, da yadda suka karkasa su gida-gida, wasu suna yin burus da su, wasu kuma su ɗaukaka su, su kambama su har ya zuwa matsayin bauta da allantarwa.

Kuma har ila yau, littafin zai yi bayanin ma'anar Ahalul Baiti a mahangar Ahalus Sunna, da yadda suke ɗaukar su, da yadda suke ƙaunar su, suna girmama su, suna yin koyi da su kamar yadda suke yin koyi da Sahabbai, kuma ba sa bambance wa tsakanin su, watau su rungumi wasu, wasu kuwa su jefa su a kwandon shara kamar yadda 'yan Shi'a suke yi.

Sa'an nan daga bisani, littafin zai ƙyale mai karatu ya yi hukunci shi da kansa a kan wane tafarki ne ya fi dacewa da Shari'a a wajen muamalantar iyalin gidan Annabi(SAW), Ahalul Baiti: tafarkin 'yan Shi'a ko na Ahalus Sunna?

Kuma a nan, kafin mu rufe wannan gabatarwa, muna tuna wa mai karatu cewa, kamar yadda muka saba a rubuce-rubucen mu, za mu dogara kacokan a kan littafan malaman Shi'a wajen bayanin mahangar su da ra'ayinsu, kamar yadda za mu dogara da littafan malaman Sunna a wajen bayanin mahangar su da ra'ayinsu. Za mu yi haka domin tabbatar da adalci wanda Allah ya yi umarni da shi, kuma domin yanke hujja da bayanin mahajja.

Muna roƙon Allah Maɗaukaki ya ɗora mu a kan sawaba, ya sanya ihilasi a cikin ayyukan mu da maganganun mu, kuma ya amfani Musulmi da wannan ɗan ƙaramin aiki. Allah shi ne abin dogaro.

# Babi Na Ɗaya

## Ahalul Baiti a mahangar Ahalus Sunna

Da farko, za mu fara gabatar da bayani a kan Ahalul Baiti daga mahangar Ahalus Sunna, kafin daga bisani mu juya ga mahangar 'yan Shi'a don mu gwada mu ga bambanci. Kuma abinda duk za mu ƙarrara a nan zai fito daga littafan malaman Sunna sanannu, waɗanda suka shahara da cewa su mabiya Sunnar Annabi(SAW) ne kuma masu ƙin bidi'a.

## Ma'anar Ahalul Baiti A Wajen Ahalus Sunna

Asalin kalmar ***ahalu*** tana nufin matar mutum, kuma tana nufin ɗaya ko da yawa (watau kalmar *tilo* ce kuma *jama'u* a lokaci guda). Ita kuwa kalmar ***baiti*** abinda take nufi gida. Idan aka ce ahalul baiti na mutum to ana nufin mutanen gidansa wanda ya haɗa da matansa da 'ya'yansa da dukkan waɗanda suke gidan na zuri'a da makusanta.

Akwai kuma ɗaya kalmar mai kama da wannan kuma mai ma'anarta, watau ***alu,*** ko kuma kamar yadda muke faɗi da Hausa: ***alaye.*** Waɗannan kalmomi biyu ma'anarsu ɗaya, ba bambanci. Amma idan aka danganta waɗannan kalmomi ga Annabi(SAW), aka ce Ahalu Baitinsa ko kuma Alayensa, to malamai sun yi saɓani dangane da ma'anarsu, ko kuma mu ce dangane da waɗanda suka ƙunsa daga cikin iyalin Annabi(SAW) da zuri'arsa.

Ra'ayi na farko. Masu wannan ra'ayi suna ganin cewa Ahalul Baiti, ko kuma Alaye, su ne waɗanda sadaka ta haramta a kansu. Dalilin masu wannan ra'ayi shi ne hadisin da Imamul Bukhari ya ruwaito cewa, "Manzon Allah(SAW)

ya kasance ana kawo masa dabino lokacin girbinsa; sai wannan ya kawo dabino, wancan ya kawo dabino har ya taru ya yi tsibi. Sai Hassan da Hussaini (suna yara) su riƙa yin wasa da dabinon. (Wata rana) ɗayansu ya ɗauki dabino guda ya sa a bakinsa. Sai Manzon Allah(SAW) ya gan shi, sai ya fitar da dabinon daga bakinsa, sa'an nan ya ce, "Ba ka san cewa Alayen Muhammadu ba sa cin sadaka ba?!"[1]

Wannan hadisi ya nuna a fili cewa Hassan da Hussaini suna cikin Alayen Annabi, watau Ahalul Baiti nasa. Amma su ke nan su kaɗai su ne Ahalul Baiti ko kuwa? A'a, akwai wasu bayan su. Bayanin hakan kuwa an same shi a cikin hadisin da Imam Muslim ya ruwaito cewa, "Abdul Muɗɗalib ɗan Rabi'a ya ba da labari cewa babansa Rabi'a ɗan Harisa ɗan Abdul Muɗɗalib da shi da Abbas ɗan Abdul Muɗɗalib sun faɗa wa Abdul Muɗɗalib ɗan Rabi'a da Falalu ɗan Abbas, Allah ya yarda da su, (suka ce): Ku tafi wurin Manzon Allah(SAW) ku ce masa: Ka saka mu cikin masu aikin tattara sadaka. Sai ya ce musu: Waɗannan sadakokin dattin mutane ne kawai, kuma lalle ba sa halasta ga Muhammad da Alayen Muhammad."[2]

Wannan hadisi yana nunawa a bayyane cewa ba 'ya'yan Annabi ne kawai, ko jikokinsa, su ne Ahalul Baiti ba, a'a har ma da baffanninsa da 'ya'yayensu. Domin su waɗannan mutane guda biyu da aka ambata a cikin hadisin cewa sun tambaye shi ya saka su cikin masu aikin tattara zakka, watau Abdul Muɗɗalib ɗan Rabi'a da Falalu ɗan Abbas 'ya'yan baffanninsa ne, guda abokin wasansa ne, gudan kuma ɗan abokin wasansa ne. Saboda haka, ɗaya ƙani ne, ɗayan kuma ɗa ne a wajensa. (Abdul Muɗɗalib da aka ambata a hadisin an sa masa sunan kakansa ne na biyu.)

[1] A duba **Sahihul Bukhari. Muslim** ma ya fitar da irinsa.
[2] A duba **Sahihu Muslim.**

Wannan shi ne ra’ayin malamai kashi na farko, cewa ‘ya’yan Annabi(SAW) da jikokinsa da baffanninsa da zuri’arsu su ne Ahalul Baiti. Daga cikin masu wannan ra’ayi akwai Abu Hanifa da Shafi’i da Ahmad binu Hanbal da wasu malaman mazhabar Malikiyya.[1]

Ra’ayi na biyu. Masu wannan ra’ayi suna ganin cewa alayen Annabi(SAW) su ne ‘ya’yansa da jikokinsa da kuma matansa na aure kawai. Sun kafa hujja da hadisai guda biyu. Na farko hadisin Humaidin Assa’idi cewa Sahabbai sun tambayi Annabi(SAW) ya za su yi masa salati? Sai ya ce, “Ku ce: Ya Allah ka yi tsira ga Muhammad da matayensa da zuri’arsa kamar yadda ka yi tsira ga Ibrahim, kuma ka yi albarka ga Muhammad da matayensa da zuri’arsa kamar yadda ka yi albarka ga Ibrahim, lalle kai ne abin godewa, mai girma.”[2] Na biyu hadisin da yake cewa, “Ya Allah ka yi tsira ga Muhammad da alayen Muhammad.”[3] Suka ce hadisi na biyu ya fassara na farkon, kuma ya nuna ƙarara cewa matan Annabi(SAW) da zuri’arsa su ne alaye, ko kuma Ahalul Baiti nasa. Yawancin malaman Malikiyya suna cikin masu wannan ra’ayi, kuma shi ne zaɓin manyan malamai, ciki har da Ibnu Taimiya, Allah ya rahamshe su baki ɗaya.[4]

Wannan ra’ayi yana da ƙarfi ainun kuma masu shi suna da hujjoji ƙarfafa da dalilai masu yawa, bayan waɗanda muka ambata a sama. Daga cikinsu akwai hadisin Innar Muminai A’isha, Allah ya ƙara mata yarda, ta ce, “Alayen Muhammad ba su taɓa ƙoshi da gurasa tare da abin tsomi (miya ko romo) ba kwana uku a jere, har ya koma ga Allah mai girma da ɗaukaka.”[5] A wannan hadisi, Innarmu A’isha, Allah ya ƙara mata yarda, tana ba mu labarin yanayin rayuwar

[1]A duba **Almuntaqa** sharhin **Muwadda** na Abul Walid Sulaiman binu Khalaf Albaji, bugun Darul Kitabil Islami, Sa’udiyya, ba tarihi, mujalladi na 2, shafi na 153.

[2] **Bukhari** da **Muslim.**

[3] ***Bukhari*** da ***Muslim.***

[4] A duba **Attamhid** sharhin **Muwadda** na Abu Umar Yusuf binu Abdillah binu Abdil Barri, bugun Wazaratu Umumil Awqaf, Maroko, 1384, mujalladi na 17, shafi na 303.

[5] **Sahihul Bukhari.**

iyalin Annabi(SAW) da irin abincin da ake ci a gidansa. Kuma ta yi amfani da kalmar *alu,* ko kuma alaye, wacce babu shakka ta haɗa da matansa da 'ya'yansa.

Har yau, masu wannan ra'ayi sun kafa hujja da aya, faɗin Allah Maɗaukaki, "Ya matan Annabi! Ba ku zama kamar kowa ba daga mata, idan kun yi taƙawa, saboda haka, kada ku sassautar da magana, har wanda ke da cuta a cikin zuciyarsa ya yi ɗammani, kuma ku faɗi magana ta alheri. Kuma ku tabbata a cikin gidajenku, kuma kada ku yi fitar gaye-gaye irin fitar gaye-gaye ta jahiliyar farko. Kuma ku tsaida sallah, kuma ku bayar da zakka, kuma ku yi ɗa'a ga Allah da Manzonsa. Allah na nufin ya tafiyar da ƙazanta kawai daga gare ku, ya mutanen Babban Gida (Ahlal Baiti). Kuma ya tsarkake ku tsarkakewa." (Suratul Ahzab: 32-33). Suka yi bayani cewa, waɗannan ayoyi waɗanda suke magana da matan Annabi kai tsaye sun kira su Ahalul Baiti, saboda haka duk wanda ya shiga ƙarƙashin wannan suna to bayansu yake bi. Kuma wannan magana haka take idan aka duba ta a hankalce; domin matan mutum su ne haƙiƙanin mutanen gidansa, saboda ko 'ya'yan mutum wannan sifa ba ta lazimtar su a ko da wane lokaci; domin suna iya ficewa daga gidan (su zama ba mutanen gidan ba) imma zuwa gidajen aure idan 'ya'ya mata ne ko kuma su yi gidan kansu idan maza ne. Matan mutum kuwa su ne mutanen gidansa na har abada.

Muna ƙara karfafa wannan ra'ayi, muna bayyana hujjojinsa a fili, saboda mai da martani ga 'yan Shi'a waɗanda suke ganin cewa matan Annabi(SAW), Allah ya ƙara musu yarda, ba sa cikin Ahalul Baiti, kamar yadda za mu gani a nan gaba kaɗan in Allah ya yarda.[1]

Ra'ayi na uku. Masu wannan ra'ayi suna ganin cewa, alayen Annabi(SAW), watau Ahalul Baiti, su ne mabiyansa dukkaninsu baki ɗaya har zuwa ranar

[1] Domin karin bayani, sai a duba **Aljami'u li Ahkamil Qur'an** na Imam Qurdubi, bugun Darush Sha'ab, Alqahira, 1372, mujalladi na 2, shafi na 290.

Alƙiyama. A wajen masu wannan ra’ayi duk Musulmi Ahalul Baiti ne domin ma’anar alu, ko kuma alaye, a wajensu shi ne mabiya. Daga cikin dalilansu sun kafa hujja da waɗannan ayoyi: faɗin Allah Maɗaukaki, “Wuta ana gitta su a kanta, safe da maraice, kuma a ranar da Sa’a take tsayawa, ana cewa: Ku shigar da mutanen Fir’auna (alu Fir’auna) a mafi tsananin azaba.” (Suratu Gafir: 46). Da faɗinsa Maɗaukaki, “Lalle mun aika iskar tsakuwa a kansu, face mabiyan Luɗu (alu Luɗin), mun tserar da su a lokacin asuba.” (Suratul Kamar: 34). Suka ce a cikin waɗannan ayoyi biyu an yi amfani da lafazin *alu Fir’auna* da *alu Luɗin* ana nufin mabiyan Fir’auna da mabiyan Annabi Luɗu(AS), wanda yake nuna ma’anar alu shi ne mabiya. Daga cikin masu wannan ra’ayi akwai wasu ‘yan mazhabar Shafi’iyya, ciki har da mashahurin malamin nan, Imam Annawawi mai littafin *Arba’una Hadisan.*

Akwai wasu ra’ayoyi dangane da ma’anar Ahalul Baiti banda waɗanda muka zana, amma ba za mu tsawaita da ambatonsu ba. Za mu taƙaita a kan uku da muka rattaba saboda ƙarfin hujjojinsu, musamman ma ra’ayi na tsakiya wanda shi ne zaɓin manyan malamai. Saboda haka, ma’anar Ahalul Baiti a wajen Ahalus Sunna su ne matan Annabi(SAW) da zuri’arsa, watau ‘ya’yansa da jikokinsa, haka zalika baffanninsa da zuri’o’insu waɗanda suka karɓi Musulunci. Duk wata falala da baiwa da daraja wacce ta keɓanci alaye to ta game waɗannan duka, kuma duk sa’ad da Musulmi ya yi salati ga alaye tare da Annabi(SAW) to a gare su duka salatin yake faɗawa.

## Matsayin Ahalul Baiti A Wajen Ahalus Sunna

Ahalus Sunna suna ɗaukar Ahalul Baiti a matsayin Musulmi na gari, masu baiwa da ɗaukaka, waɗanda Allah ya zaɓe su, ya keɓance su da falala da baiwa

saboda kusancinsu da Annabi(SAW). Saboda haka suna girmama su irin girman da ya cancance su a Shari'a, ba tare da azarɓaɓi ko wuce gona da iri ba, kuma suna ƙaunar su saboda sonsu son Annabi ne, kuma son Annabi son Allah ne.

Waɗanda suke a cikinsu Sahabbai ne, kamar Ali da Faɗima da Hassan da Hussaini da Aisha da Hafsa da Abbas da ɗansa Abdullahi, da Ja'afar da Aƙilu da sauransu, to waɗannan suna ba su daraja biyu: kasancewarsu Sahabbai kuma kasancewarsu Ahalul Baiti. Waɗanda kuma ba Sahabbai ba ne, ba su rayu tare da Annabi ba, kamar sauran 'ya'yan Faɗima ƙanana Ruƙayya da Ummu Kulthum, da sauran 'ya'yan Ali waɗanda ya haifa da wasu matan nasa dabam, irin su Muhammad binul Hanafiyya da 'yan uwansa, da sauran zuri'o'in baffanin Annabi(SAW) da 'yan uwansa: zuri'ar Abbas, zuri'ar Hamza, zuri'ar  Aƙilu, zuri'ar Ja'afar, da sauransu, to waɗannan ana ba su darajarsu da Allah ya ba su ta kusanci ga Annabi(SAW) da haɗa dangantakar jini da shi. Haka nan kuma, Ahalus Sunna suna yin salati ga Ahalul Baiti tare da Annabi(SAW) a duk sa'ad da suka yi masa salati.

Ahalus Sunna suna son Ahalul Baiti so irin na Musulunci, so na Shari'a, ba so na jahiliyya ba. Saboda haka, ba sa wuce makaɗi da rawa a wajen ƙaunar su da girmama su. Ba sa dangana musu almarori, ko su ƙudure cewa suna da wani kayan gado na annabta wanda suka keɓanta da shi koma bayan sauran Musulmi, ko su ce sun san gaibu, ko kuma su kaɗai suka cancanci khilafa, da sauran irin waɗannan ƙudure-ƙudure na masu addini da jahilci ko son zuciya. A wajen mu'amala da Ahalul Baiti, Ahalus Sunna suna tsayawa a kan koyarwar Alƙur'ani da Sunna, ba sa wucewa ko taƙi ɗaya.

## Haƙƙoƙin Ahalul Baiti a kan Musulmi

Ahalus Sunna suna ƙudure cewa, Ahalul Baiti Allah ya ƙara musu yarda baki ɗaya, suna da haƙƙoƙi a kan ko wane Musulmi waɗanda yake wajibi ne a kiyaye da su, kuma a bayar da su ta fuskar da ta kamata. Waɗan nan haƙƙoƙi sun haɗa da:

1. Kaunar su da jiɓintar su da ba su girma, saboda faɗin Allah Maɗaukaki, "Ka ce (ya Muhammad): Ba na tambayar ku wata ijara a kansa (iyar da aike), face dai soyayya ta cikin zumunta." (Suratush Shura: 23) Ibnu Kathir ya bayyana cewa, daga cikin ma'anonin ayar tana nufin, "Ku so ni ta hanyar son makusantana. Watau ku kyautata musu." Kuma ya dangana ruwayar haka ga Imam Bukhari.[1]
2. Yin salati a gare su tare da Annabi(SAW), watau haɗawa da su a salati duk sa'ad da aka yi masa. Kuma ana iya yin salati ga ɗayansu yayin da aka ambace shi shi kaɗai.
3. Ba su kaso daga khumusi (watau kashi ɗaya bisa biyar) na ganima, saboda faɗin Allah Maɗaukaki, "Kuma ku sani cewa, abin da kuka sami ganima daga wani abu, to, lalle ne Allah yana da humusinsa kuma don Manzo, kuma saboda masu zumunta." (Suratul Anfali: 41) Ibnu Kathir ya ce malamai masu yawa suna ganin kason masu zumunta ana ba da shi ga Banu Hashim da Banul Muɗɗalib.[2]
4. Kuduri mai ƙarfi da cewa nasabar Annabi(SAW) ita ce mafi ɗaukakar nasaba, kuma danginsa su ne mafi darajar dangi.
5. Kare su da tsare mutuncinsu da kuɓutar da su daga ƙarerayin da aka laƙa musu a bisa jahilci ko son zuciya. Misali irin ƙarerayin da malaman Shi'a

[1] Duba **Tafsiru Ibni Kathir** na Abul Fida Isma'il binu Kathir, bugun Maktabatus Safa, Alqahira, 1423/2002, mujalladi na 7, shafi na 123.
[2] Duba **Tafsiru Ibni Kathir**, mujalladi na 4, shafi na 37.

suke laƙa musu na abubuwan da suka saɓa da abinda kakansu, Manzon Allah(SAW), ya zo da shi na haske da shiriya dake cikin Kur'ani da Sunnah.

Muhimmyar Faɗakarwa: Waɗan nan haƙƙoƙi da aka ambata suna tabbata da sharuɗɗa biyu: Musulunci da tabbatar nasaba. Watau mutum sai nasabarsa ta tabbata cewa ya haɗa jini da Annabi(SAW), kuma ya karɓi Musulunci sa'an nan yake cancantar waɗan nan haƙƙoƙi.

# Babi Na Biyu

# Ahalul Baiti a mahangar 'Yan Shi'a

Bayan mun ga ma'anar Ahalul Baiti da matsayinsu a wajen Ahalus Sunna, bari a yanzu mu karkata akalar alƙalami zuwa ga ra'ayin 'yan Shi'a da ƙudurinsu dangane da waɗan nan zaɓaɓɓun bayi da yadda suka ɗauke su. Kuma, kamar yadda muka faɗi a gabatarwa, za mu dogara kacokan wajen rubuta wannan babin a kan littafan malaman Shi'a waɗanda suka shahara kuma Rafilawa a ko ina a duniya suke izna da ilminsu da maganganunsu.

## Ma'anar Ahalul Baiti A Wajen 'Yan Shi'a

A wajen 'yan Shi'a, Faɗima da Ali da 'ya'yansu Hassan da Hussaini, Allah ya ƙara musu yarda baki ɗaya, da zuri'o'insu su kaɗai su ne Ahalul Baiti. Sun gina wannan ra'ayi nasu a kan wani hadisi da suke ruwaitowa cewa, Innar Muminai Ummu Salmah, Allah ya ƙara mata yarda, ta ce, "Ayar 'Allah na nufin ya tafiyar da ƙazanta kawai daga gare ku, ya mutanen Babban Gida, kuma ya tsarkake ku tsarkakewa' ta sauka a ɗakina ina zaune kusa da ƙofa, sai na ce: Ya Ma'aikin Allah, ni ba na cikin mutanen Babban Gida? Sai ya ce: 'Ke kina bisa alheri, ke kina cikin matan Annabi(SAW).' Ta ce: A cikin ɗakin Manzon Allah da Ali da Faɗima da Hassan da Hussaini suna zaune, sai (Annabi) ya lulluɓe su da wani tufafi, sa'an nan ya ce, 'Ya Ubangiji, waɗannan su ne iyalin gidana, ka tafiyar da ƙazanta daga gare su kuma ka tsarkake su tsarkakewa."

Wannan hadisi malaman Ahalus Sunna sun ruwaito irinsa amma banda ƙarin da aka ce wai Innar Muminai Ummu Salmah, Allah ya ƙara mata yarda, ta tambayi

Annabi(SAW) ko ita ba ta cikin Ahalul Baiti, ya ce e. Wannan ƙarin bai inganta ba.[1]

Amma su 'yan Shi'a sun yarda da wannan ƙarin, kuma a dalilinsa ne suka kore matan Annabi(SAW) daga cikin Ahalul Baiti. Sai dai ba Uwayen Muminai kawai suka kore ba, sun ma kore har da wasu 'ya'yan Faɗima ɗin. Faɗima ta haifawa Ali 'ya'ya huɗu. Su ne Hassan da Hussaini da Ruƙayya da Ummu Kulthum. Ruƙayya ta rasu tana ƙarama, amma Ummu Kulthum ta girma kuma ubanta ya aura wa Sarkin Musulmi Umar ita, har ta haifa masa ɗa mai suna Zaidu, kuma tana cikin matansa da suka yi masa takaba. Shi wannan ɗan Zaidu ya girma amma bai haihu ba.

Sa'an nan 'yan Shi'a sun kore sauran ɗiyan Annabi duka, maza da mata, da zuri'o'insu daga jimillar Ahalul Baiti. Kamar yadda suka kore dukkan baffanin Annabi da zuri'o'insu.

Kai a cikin malaman Shi'a ma akwai waɗanda suka ce Annabi(SAW) ba shi da ɗiya mace sai Faɗima kawai. Suka ce wai Zainab da Ruƙayya da Ummu Kulthum duka agololinsa ne; 'ya'yan Nana Hadiza ne da ta haifa da mijinta na farko.[2] Wasu malaman nasu ma sun wuce nan, suka ce wai Hadiza ma ba haihuwarsu ta yi ba, riƙa su tayi![3] Kuma duka wannan sun yi haka ne don su kore wa Sayyidina Usman(RA) auren 'ya'yan Manzo biyu, watau Ruƙayya da Ummu Kulthum, Allah ya ƙara musu yarda, wanda hakan ya tabbata a tarihi kuma a dalilinsa ne ya samu laƙabin Zun Nuraini. Amma ina rowan 'yan Shi'a da tarihi, kuma ina ruwansu da ilmi?! Su kawai son zuciyarsu suka sani. Allah ya shirye su.

---

[1] Imam Ahmad da Tirmizi sun ruwaito hadisin daga Ummu Salmah(RA) kuma Imam Muslim ya ruwaito shi daga A'isha(RA). Duba bayani kan hadisin a cikin **Tafsiru Ibni Kathir,** mujalladi na 6, shafi na 193-195.

[2] Domin wannan karyar ta rashin albarka, duba littafin **Da'iratul Ma'arifish Shi'iyya** na babban malaminsu, Hassan Amin, bugun Darut Ta'aruf, Bairut, ba tarihi, 1/50.

[3] Domin wannan karyar ta rashin kunya, duba littafin **Al'istigatha fi Bida'is Thalatha** na babban malaminsu Abul Qasim Ali binu Ahmad Alkufi, bugun Darul Kutubil Ilmiyya, Qum-Iran, ba tarihi, shafi na 108.

Babu shakka akwai abin ta'ajibi dangane da ma'anar Ahalul Baiti a wajen 'yan Shi'a. Su a wajensu Ali da Faɗima da 'ya'yansu guda biyu kawai, banda sauran, su ne Ahalul Baiti. To me ya sa ba sa maganar Ummu Kulthum, ba sa lasafta ta a cikin Ahalul Baiti alhali kuwa ita ma ɗiyar Faɗima da Ali ce kamar Hassan da Hussaini ba bambanci? Kuma ta ya za'a yi maganar mutanen gidan mutum amma a ce matansa ba sa ciki? Wane irin gida ne za'a ce matan gidan ba mutanen gidan ba ne, sai 'ya'ya ne kawai mutanen gidan? Wannan hukunci ya saɓa wa hankali da al'ada kamar yadda ya saɓa wa nassoshin Shari'a. Abu guda kawai wannan hukunci ya dace da shi, shi ne son zuciya wanda 'yan Shi'a suka gina yawancin addininsu a kai.

Wani abin mamakin kuma shi ne, ko a cikin 'ya'yan Faɗima ɗin, su 'yan gaban goshin, banda Ummu Kulthum wacce suka jefar a juji, ko su 'yan gaban goshin a cikinsu akwai wasu zaɓaɓɓu fiye da wasu. 'Ya'yan Hussaini sun fi 'ya'yan Hassan ƙima, kuma a cikinsu ne ake da imamai tara tsaba, ko kuma goma in mun haɗa har da ubansu Hussaini. Shi kuwa Hassan shi kaɗai shi ne imami, amma a cikin zuri'arsa babu imami ko ɗaya. Don me ya sa aka samu wannan bambanci? Babu dalili, ba hujja sai son zuciyar 'yan Shi'a kawai wanda, kamar yadda muka faɗi a baya kaɗan, shi ne tushe da suka gina addininsu a kai.

Duba ka gani, mai karatu, yadda Shaiɗan yake wasa da hankalin 'yan Shi'a. Ɗiyan Faɗima, Allah ya ƙara mata yarda, su kaɗai su ne Ahalul Baiti. Kuma a cikinsu banda Ummu Kulthum. Kuma, har yau, a cikin zaɓaɓɓun, watau Hassan da Hussaini, zuri'ar Hussaini suke da imamai, duk da cewa shi ne ƙani, amma zuri'ar Hassan ba imami ko ɗaya a cikinsu.

Mutane masu aiki da hankali suna tambaya: Da wane dalili 'ya'yan Hussaini suka fi 'ya'yan Hassan? Babu amsa mai gamsarwa sai ko hasashen tasirin

Majusanci na mutanen Iran. Tarihi ya tabbatar da cewa, a zamanin Sarkin Musulmi Umar binul Khaɗɗabi, bayan an ci daular Majusawa ta Farisa (Iran) da yaƙi, Musulmi sun ci ganimar dukiyoyi da mataye. Daga cikin wannan ganima, Umar ya baiwa Hussaini(RA) kyautar 'yar Sarkin Farisa mai suna Shaharbano wacce Hussaini ɗin ya mayar da ita sa-ɗaka. Wannan gimbiya kuma kwarkwara ita ce ta Haifa wa Hussaini ɗansa Ali wanda ake wa laƙabi da Zainul Abidin, wanda kuma ta hanyarsa ne zuri'ar Hussaini ta ɗore.[1] To da yake yawancin 'yan Shi'a mutanen Farisa ne, sai suka laƙe wa zuri'ar Hussaini saboda 'ya'yan ɗiyarsu ne. Dalili ke nan da ya sa suka fifita su a kan zuri'ar Hassan.

Kamar yadda mai karatu yake iya gani, wannan abu (watau fifita 'ya'yan Hussaini a kan na Hassan) ba'a gina shi a kan wata hujja ko dalili ba, sai dai son zuciya kawai. To ta ƙaƙa son zuciya zai zama addini?

## Matsayin Ahalul Baiti A Wajen 'Yan Shi'a

A wajen 'yan Shi'a, Ahalul Baiti, kamar yadda suka fahimce su, su kaɗai su ne Musulmi kuma babu mai zama Musulmi sai wanda yake son su kuma yake jiɓintar su, jiɓinta da so waɗanda suka dace da fahimtar Rafilawa. A kan wannan ne suka gina aƙidarsu cewa Sahabbai duka sun yi ridda bayan rasuwar Annabi(SAW) sai mutum bakwai kawai. Waɗannan mutane su ne Miƙdad binul Aswad, Abu Zarrin Algifari, Salman Alfarisi, Ammar binu Yasir, Abu Sasan Al'ansari, Huzaifa binul Yaman da Abu Amra, Allah ya ƙara musu yarda.[2] Waɗannan Sahabbai bakwai da 'yan Shi'a suka yarda da Musuluncinsu, babu abinda ya raba su da sauran Sahabbai 'yan uwansu sai kawai cewa sun yi ƙaurin

[1] Babban malamin Nasaba dan Shi'a, Ibnu Anbata, ya tabbatar da wannan a cikin littafinsa, **Umdatud Dalib fi Ansabi Aali Abi Dalib,** 192.
[2] A duba babin Akidar 'Yan Shi'a dangane da Sahabbai a cikin littafinmu **Bacin Tafarkin 'Yan Shi'a da Akidojinsu.**

suna da kasancewa su masoyan Ali binu Abi Ɗalib ne kuma sun goyi bayansa a rikicin da ya faru tsakaninsa da Mu'awiyya binu Abi Sufyan. Wannan yana nuna cewa, a ganin 'yan Shi'a, ba Musulmi sai Ahalul Baiti, sai kuma waɗanda suka bi su, suka jiɓince su. Don haka ne suka sanya imani da imamai a matsayin ɗaya daga shika-shikan Musulunci. Babban malamin Hadisi a wajen 'yan Shi'a, Muhammad binu Ya'aƙub Alkulaini, ya ruwaito Abu Ja'afar, imamin Rafilawa na shida, yana cewa: "An gina Musulunci a kan abubuwa guda biyar: sallah da zakka da hajji da azumi da wilaya (watau imama)."[1] Idan mai karatu ya kula zai ga cewa, a cikin wannan ruwaya ta 'yan Shi'a imama ta maye makwafin Kalmar Shahada wacce ba'a ambace ta ba. To imama, a wajen 'yan Shi'a, ita ce Kalmar Shahada kuma sun kawo ambatonta a ƙarshe domin ɓad da bami.

Don haka, matsayin Ahalul Baiti a wajen Rafilawa ya wuce a ce wai su zaɓaɓɓu ne, ko masu girma, ko masu falala a addini. A'a, sun wuce nan! Ahalul Baiti a wajen 'yan Shi'a su ne addinin kansa. Don su aka halicci duniya da lahira, suna sama da annabawa da manzanni da mala'iku makusanta, don haka ya wajaba a bauta musu. Wannan zai bayyana a fili idan muka yi darasun matsayin imamai a wajen Rafilawa.

## Matsayin Imamai A Wajen 'Yan Shi'a

Matsayin imamai a wajen 'yan Shi'a babu sama da shi, domin suna aza su a bisa da annabawa da manzanni, kuma a wani yayi su ba su sifofin allantaka.

'Yan Shi'a suna ɗaukar imamai a matsayin ma'asumai, waɗanda ba sa kuskure kuma ba sa aikata zunubai ƙanana ko manya, kamar annabawa da manzanni ba bambanci. Saboda haka, ba sa mantuwa, ba sa tuntuɓe, ba sa sha'afa,

[1] **Usulul Kafi** na Muhammad binu Ya'aqub Alkulaini, bugun Darul Kutubil Islamiyya, Teheran-Iran, ba tarihi, mujalladi na 2, shafi na 18.

ba sa rafkanuwa. Dangane da wannan, wani babban malaminsu da ake kira Muhammad binu Nu'uman Almufid, yana faɗin, "Lalle imamai waɗanda suke tsaye matsayin annabawa wajen zartar da hukunce-hukunce da tsai da haddoji da tsare shari'o'i da ladabtar da talikai ma'asumai ne kamar ismar annabawa, kuma bai yiwuwa su yi rafkanuwa a cikin wani lamari na addini, kuma ba sa mance wani abu na hukunce-hukunce."[1] Wani malamin nasu mai suna Abu Ja'afar Muhammad binu Ali binu Hussain binu Musa binu Babawaihi Alƙummi (wanda aka fi sani da laƙabin Assaduƙ) yana cewa, "Kudurinmu dangane da annabawa da manzanni da imamai shi ne cewa su ma'asumai ne, tsarkaka ne daga dukkan wani datti. Kuma cewa su ba sa aikata zunubi ƙarami ko babba, kuma ba sa saɓawa Allah abinda ya umarce su kuma suna aikata abinda aka umarce su. Wanda ya kore musu isma dangane da wani abu na lamarinsu to haƙiƙa ya jahilce su, kuma wanda ya jahilce su to shi kafiri ne."[2]

'Yan Shi'a Rafilawa suna ƙudure cewa imamansu sun san gaibu, kuma suna da sanin abinda ya faru tun farkon halitta da abinda zai faru har zuwa ranar Alƙiyama. Malaminsu Kulaini ya ruwaito daga imaminsu na shida, Abu Abdillahi, ya ce, "Na rantse da Ubangijin Ka'aba, na rantse da Ubangijin wannan ginin (Ka'aba) -ya maimaita sau uku- da na kasance tare da (Annabi) Musa da Haliru da na faɗa musu cewa ni na fi su sani, da na ba su labarin abinda ba su sani ba; domin Musa da Haliru(AS) an ba su sanin abinda ya kasance ne (kawai) amma ba'a ba su sanin abinda zai zo da abinda zai kasance ba har zuwa ranar Alƙiyama. Mu kuwa (watau imamai) mun gaji wannan ilmi daga Manzon Allah gado na haƙiƙa."[3] Malaminsu, Muhammad binu Nu'uman Almufid, ya tabbatar da wannan aƙida

[1] A duba **Awa'ilul Makalat** na Muhammad binu Nu'uman Almufid, bugun Darul Kitabil Islami, Bairut, 1403/1983, shafi na 71-72.
[2] A duba **Aka'idul Ithnai Ashariyya** na Ibrahim Almusawi Alzanjani, bugun Muassasatul Wafa, Bairut, ba tarihi, mujalladi na 2, shafi na 157.
[3] **Usulul Kafi** na Muhammad binu Ya'aqub Alkulaini, mujalladi na 1, shafi na 261.

tasu. Ya ce, “Imamai daga zuri’ar (Annabi) Muhammad (SAW) sun kasance suna sanin abinda yake ɓoye cikin zukatan wasu bayi, kuma sun san abinda zai kasance kafin kasancewarsa.”[1]

‘Yan Shi’a suna ƙudure cewa wahayi yana sauka ga imamansu. Domin tabbatar da haka, sun ruwaito daga imaminsu Abu Abdillahi, ya ce, “Mu ana ba mu guzuri (na ilmi) dare da rana, kuma ba don ana ba mu guzuri ba da abinda yake gare mu (na ilmi) ya ƙare. (Mai ruwaya) Abu Basir ya ce: Allah ya sanya ni fansar ka, wane ne yake zuwa muku? Ya ce: Daga cikinmu akwai wanda yake gani da ido ƙuru-ƙuru; daga cikinmu akwai wanda yake ji da kunnensa amo kamar amon sarƙa a cikin tasa. (Mai ruwaya) ya ce: Na ce: Allah ya sanya ni fansarka, waye yake zuwa muku da wannan? Ya ce: Wani halitta ne wanda ya fi Jibirilu girma.”[2] Mai karatu yana iya gani cewa wannan ruwaya ba ta bar wani yanayi na saukar wahayi ga annabawa da manzanni ba face ta tabbatar da shi ga imamai.

Har ila yau, ‘yan Shi’a suna wuce gona da iri wajen son imamansu da girmama su da kambama su har su fifita su a kan annabawa da manzanni da mala’iku makusanta ga Ubangiji. Ya zo a cikin irin ruwayoyin da suke danganawa ga Annabi(SAW) cewa wai ya ce da Ali(RA): “Lallai Allah mai girma da ɗaukaka ya fifita annabawansa manzanni a bisa mala’iku makusanta, kuma ya fifita ni a kan dukkanin annabawa da manzanni. Ya kai Ali, fifiko a bayana ya tabbata a gare ka da imamai masu zuwa a bayanka.”[3] A cikin wani littafin nasu mai suna *Haƙƙul Yaƙin fi Usulid Din*, mai littafin, Abdullahi binu Shabbar, yana cewa, “Ya wajaba a yi imani cewa Annabinmu da alayensa ma’asumai suna da fifiko a kan annabawa

[1] **Awa’ilul Makalat** na Muhammad binu Nu’uman Almufid, shafi na 75.
[2] **Biharul Anwar** na Muhammad Baqir Almajalisi, bugun Muassasatul Wafa, Bairut, ba tarihi, mujallaadi na 26, shafi na 53.
[3] A duba **Ilalush Shara’i’i** na Muhammad binu Babawaihi Alqummi Assaduk, bugun Almaktabatul Haidariyya, Najaf-Iraq, shafi na 5.

da manzanni da mala'iku makusanta saboda hujjoji masu yawan gaske da suka zo da haka."[1]

Banda wannan duka, Rafilawa suna tabbatar wa da imamansu sifofin allantaka. Daga cikin irin abubuwan da suke danganta wa Ali binu Abi Ɗalib(RA) akwai wannan ruwaya cewa wai ya ce, "Ni ne idanun Allah; ni ne hannun Allah; ni ne ƙofar Allah." A wata ruwayar kuma ya ce, "Ni ne ilmin Allah; ni ne zuciyar Allah mai kiyayewa; ni ne harshen Allah mai furuci; ni ne idanun Allah masu gani; ni ne haƙarƙarin Allah; ni ne hannun Allah."[2]

Dangana irin waɗannan ruwaroyi na ƙarya bai tsaya kan Ali ba kawai, a'a har ma ga Annabi(SAW) suna danganawa. Sulaim binu Kais ya ruwaito cewa Manzon Allah(SAW) ya faɗi ga Ali kamr haka: "Ya Ali, kai kana daga gare ni, ni ina daga gare ka. An gauraya namanka da namana, da jininka da jinina…. Wanda ya yi musun wilayarka ya yi musun allantakar Allah. Ya Ali, kai ne tutar Allah mafi girma a bayan ƙasa bayana, kuma kai ne bango mai girma a ranar Alƙiyama. Wanda ya shiga inuwarka ya rabanta domin hisabin talikai duka yana hannunka kuma makomarsu na gare ka. Mizani naka ne; siraɗi naka ne; taron Alƙiyama naka ne; hisabi naka ne. Wanda ya fake da kai ya tsira kuma wanda ya saɓa maka ya halaka. Allah ka shaida, Allah ka shaida."[3]

Kamar yadda mai karatu yake iya gani, a wajen 'yan Shi'a imamai su ne komai. Suna gaba da annabawa da manzanni kuma suna tarayya da Ubangiji a allantakarsa. Wannan ya sa aka samu wasu daga cikinsu waɗanda suke bauta musu kuma suna bayyana wannan a fili ta wajen irin sunayen da suke saka wa 'ya'yansu, kamar Abdul Hussain, Abdul Amir (Amir suna nufin Ali), da sauransu.

---

[1] A duba **Hakkul Yakin fi Usulid *Din*** na Abdullahi Shubbar, bugun Darul Kitabil Islami, Bairut, ba tarihi, mujalladi na 1, shafi na 209.
[2] A duba **Basa'irud Darajat** na Muhammad binu Hassan Alsaffar, bugun Manshuratul A'alami, Teheran-Iran, 1362, shafi na 81.
[3] **Kitab Sulaim binu Qais** na Sulaim binun Qais Alkufi, bugun Manshuratul A'alami, Teheran-Iran, ba tarihi, shafi na 244-245.

Wannan ita ce aƙidar 'yan Shi'a dangane da imamai, kuma wannan shi ne yadda suka ɗauke su. Babu shakka wannan aƙida ta saɓa da Alƙur'ani mai girma da hadisan Annabi(SAW) ingantattu. Kai ta ma saɓa da hankali lafiyayye. Haka nan kuma ta saɓa da aƙidar imaman su da kansu, saboda imaman Shi'a dukkaninsu, tun daga kan Ali binu Abi Ɗalib har ya zuwa na ƙarshensu, mabiya Sunnar Annabi ne, sai dai malaman Shi'a sun laƙa musu ƙarerayi don su fake da su, su samu dammar ɓatar da al'umma.

Wannan shi ne ƙudurin Ahalus Sunna dangane da imaman Shi'a, Allah ya ƙara musu yarda, cewa duk abinda aka dangana musu wanda ya saɓa da Alƙur'ani da Sunna, to ƙarye ce ake yi musu. Muna roƙon Allah ya isr musu wannan ƙarya da ƙazafi da Yahudawa da Majusdawa suka laƙa musu.

A nan gaba, za mu ware imamai da ambato, mu yi bayanin matsayinsu a wajen Ahalus Sunna a wani littafi na musamman, in Allah ya yarda.